# Fahimta da kuma Raba Abubuwan da Wasu Ke Ji

## Labari na 1

Gabi tana wurin cin abincin rana tare da ƙawarta, amma a lokacin da ta shiga ban ɗaki, ta bar wayarta a kan tebur. A yayin da ta tafi, ƙawarta Castel ta ɗauki wayar Gabi sannan ta fara duba saƙonnin karta kwananta. Saƙon farko da ta fara gani na fushi ne wanda ya fito daga mahaifiyarta saboda ta faɗi lissafi.

- Yaya Gabi za ta ji saboda wannan?

- Me yasa Gabi ba ta so ta sanar da ƙawarta game da sakamakonta da bai yi kyau ba?

- Shin za a iya amincewa da abin da Castel ta aikata?

- Yaya sauran ƙawayensu da ke wurin cin abincin za su ji game da abun da Castel ta aikata?

- Me kake tunani game da Castel? Shin Castel ta nuna ɗabi'a mai kyau? Shin za ko sa ki yi ƙawa da Castel?

    - Yaya za ka ji idan wani ya yi maka irin wannan?

    - Shin leƙa abin wani yana da kyau? Idan fa ka damu da abokinka?

## Labari na 2

Rodrigo yana yin magana da Caitlin a lokacin da ya zame sannan ya faɗa cikin laka. Caitlin yana ganin ya zama abin dariya kuma ya ɗauki hotonsa, amma Rodrigo bai yi dariya ba saboda ya kunyata.

- Me yasa Caitlin zai aike da hoton a intanet?

- Me yasa Rodrigo ya fusata?

- Me kake ganin ya kamata Rodrigo ya ce ma Caitlin?

- Yaya za ka ji idan wani ya ɗauki hotonka da ka kunyata? Shin za ka so a sanya wannan a intanet?

- Shin wannan yanayin wani lamari ne na cin mutunci?

## Labari na 3

Victoria ɗaliba ce mai shekaru 15 tare da ƙannanta guda biyu, da mahaifiya, da

ƙawaye masu yawa da kuma abokan karatu. Victoria da Marek abokan karatun juna ne kuma suna aiki tare a kan wani aiki a ajin kimiyya. Jiya, an yi masu gwaji a ajin kimiyya, a inda kowane ɗalibi ya samu sakamakonsa. Mare ya lura cewa Victoria ta fusata sosai. Satin gaba Victoria ba za je makaranta ba na kwanaki da yawa, soboda haka dole ne Marek yayi aiki a kan aikin kimiyya shi kaɗai. A lokacin da ta dawo, ta sanar da Marek cewa sai da ta ga likita, amma ba ta ce wani abu ba kuma.

- Wane ne ya kamata ya san sakamakonta a makaranta? Tarihin ganin likitanta? Me yasa?

- Wa Victoria za ta so ta yi magana da shi game da waɗannan matsalolin?

- A rayuwarka, wasu irin misalan bayanai ne kake so iyayenka / mai ba ka kulawa su gani amma ba abokanka ba, ko wanda kake so abokanka su gani amma ba iyayenka ba?

# Fahimta da kuma Raba Abubuwan da Wasu Ke Ji: Kwafin Mai Karantarwa

## Labari na 1

Gabi tana wurin cin abincin rana tare da ƙawarta, amma a lokacin da ta shiga ban ɗaki, ta bar wayarta a kan tebur. A yayin da ta tafi, ƙawarta Castel ta ɗauki wayar Gabi sannan ta fara duba saƙonnin karta kwananta. Saƙon farko da ta fara gani na fushi ne wanda ya fito daga mahaifiyarta saboda ta faɗi lissafi.

- Yaya Gabi za ta ji saboda wannan?

    - Gabi za ta iya jin cewa an keta sirrinta kuma ta kasa amincewa da ƙawarta.

- Me yasa Gabi ba ta so ta sanar da ƙawarta game da sakamakonta da bai yi kyau ba?

    - Gabi za ta iya ganin cewa sakamakon da ta samu wani bayanin sirri ne.

- Shin za a iya amincewa da abin da Castel ta aikata?

    - Ya kamata mahalarta taron su yi la'aƙari da cewa nasu al'adun na kewaye da sirrin da ke haɗe da sakamakonsu da kuma wayoyinsu, da kuma abubuwan da suke tsammani daga wurin abokansu.

- Yaya sauran ƙawayensu da ke wurin cin abincin za su ji game da abun da Castel ta aikata?

    - Ya kamata mahalarta taron su yi la'aƙari da yanda za su mayar da martani idan suka ga wata ɗabi'ar da ba ta dace ba.

- Me kake tunani game da Castel? Shin Castel ta nuna ɗabi'a mai kyau? Shin za ko sa ki yi ƙawa da Castel?

    - Yaya za ka ji idan wani ya yi maka irin wannan?

    - Shin leka abin wani yana da kyau? Idan fa ka damu da abokinka?

        - Ya kamata a ga ɗabi'un mahalarta taron sun nuna a kan tasu al'adar da ke kewaye da sirri da kuma dangantaka ta musamman.

## Labari na 2

Rodrigo yana yin magana da Caitlin a lokacin da ya zame sannan ya faɗa cikin laka.

Caitlin yana ganin ya zama abin dariya kuma ya ɗauki hotonsa, amma Rodrigo bai yi dariya ba saboda ya kunyata.

- Me yasa Caitlin zai aike da hoton a intanet?

    - Ya kamata mahalarta taron su gane abubuwan da suka ja hankalin Caitlin: dariya ko so su ne abubuwan da aka amince da su wajen aikewa da wani abu a intanet, in dai har ba za su cutar da wani ba.

- Me yasa Rodrigo ya fusata?

    - Ya kamata mahalarta taron su yi la'akari da abubuwan da wasu za su ji a lokacin yin amfani da dandalin sadarwar zamani.

- Me kake ganin ya kamata Rodrigo ya ce ma Caitlin?

    - Ya kamata mahalarta taron su fito da wasu dabarun da za a magance wannan ɗabi'r.

- Yaya za ka ji idan wani ya ɗauki hotonka da ka kunyata? Shin za ka so a sanya wannan a intanet?

    - Ya kamata mahalarta taron su yi la'ƙari da nasu al'adun a kan abubuwan wasu da za su raba a intanet.

- Shin wannan yanayin wani lamari ne na cin mutunci?

    - Ya kamata mahalarta taron su yi la'akari da abubuwan da ke haifar da wulaƙanci sannan su tattauna wannan yanayin.

## Labari na 3

Victoria ɗaliba ce mai shekaru 15 tare da ƙannanta guda biyu, da mahaifiya, da ƙawaye masu yawa da kuma abokan karatu. Victoria da Marek abokan karatun juna ne kuma suna aiki tare a kan wani aiki a ajin kimiyya. Jiya, an yi masu gwaji a ajin kimiyya, a inda kowane ɗalibi ya samu sakamakonsa. Mare ya lura cewa Victoria ta fusata sosai. Satin gaba Victoria ba za je makaranta ba na kwanaki da yawa, soboda haka dole ne Marek yayi aiki a kan aikin kimiyya shi kaɗai. A lokacin da ta dawo, ta sanar da Marek cewa sai da ta ga likita, amma ba ta ce wani abu ba kuma.

- Wane ne ya kamata ya san sakamakonta a makaranta? Tarihin ganin likitanta? Me yasa?

    - Ya kamata mahalarta taron su yi la'akari da yanda bambancin bayani ke da matakan sirri daban-daban. Sakamakon Victoria a makaranta wani bayanin sirri ne wanda ba ta son ƙawarta, abokin karatu, ko wasu mutanen su sani. Duk da haka, ba sirri ba ne ga iyayenta / masu kula da ita. Haka ya

kasance ga tarihin lafiyarta, ko da yake wannan bayanin ya fi zama sirri sosai.

• Wa Victoria za ta so ta yi magana da shi game da waɗannan matsalolin?

- Victoria za ta so ta adana nata sirri. Ya kamata a mutunta wannan ra’ayin. Haka kuma za ta iya zaɓar ta raba wasu, amma ba duka ba, bayanin sirri. Misali, za ta iya raba wahalhalun da ta sha a makaranta da iyayenta / masu kula da ita, amma ba ƙawayenta ba.

• A rayuwarka, wasu irin misalan bayanai ne kake so iyayenka / mai ba ka kulawa su gani amma ba abokanka ba, ko wanda kake so abokanka su gani amma ba iyayenka ba?

- Ya kamata mahalarta taron su yi la’akari da nasu abubuwan da suke so dangane da sirri.

Wannan kayan karantarwar da Matasa da Kafar Watsa Labarai suka samar a Cibiyar Samar da Intanet &amp ta Berkman Klein; Jama'a a Jami'ar Harvard a ƙarƙashin lasisin Creative Commons Attribution-ShareAlike 4.0 International. Za ka iya yin amfani da wannan, har da yin kwafi da kuma shirya samar da ayyuka, ko kuɗi ko kuma wanda ba na kuɗi ba, kamar yanda ka siffanta. Matasa da Kafar Watsa Labarai a matsayin tushen da suka samar da ayyukan na ainihi da kuma raba wasu ayyukan da za su zo a gaba a ƙarƙashin sharuɗɗa ɗaya. Waɗannan da wasu ƙarin kayayyakin karantarwar su ma akwai su a intanet a Dandalin Kayayyakin Karatu da Rubutun Zamani na Berkman Klein.